**Interview 12: Ummaru Adamu, Mai Duma**

**Ummaru Adamu (UA):** To. Ni lalle ni mutumen Maraɗî ne. Kuma sunana Ummaru Adamu. E. Ni kuma inda aka haihe ni cikin Sumarāna Hàbū ƙauyen Maraɗî ne, kilo biyu da Maraɗî.
**Lori**: Mm.
OA: Amma ni mutumen Maraɗî ne. E. Sunan baba…sunan babana Adamu.

Lori: Mm.
OA: Sunan mammata Hauwa. Ni kuma sunana Ummaru.

Int: Mm.
OA: E. Sunansu, wannan ƙwarya ce ga ta. Ƙwarya ce. Wagga hwata akuya ce. Wagga ma ƙwarya ce wagga ma hwata akuya ce. Dâ lokacin dâ, ba a san, ba mu san wanga abun ba.

Int: Mm.
OA: Dâ sa'an nan hwata shanu ce muke īb…ake saye. In aka saye sai a yi, sai a, sai a yi yanka ƙanana, sai a yi yanka kankanana sai a mirɗe ta a mirɗe ta. Da gashin in aka mirɗe in ta sha iska sai a zoge gashin kawai ta koma zare kama haka. Sai a yi ɗinki. To yanzu da, abu komi na…komi na ci gaba, shina ƙara yi …shina ƙara ci gaba yanzu sai muka aje tun da in damana ta zo, in damana ta zo ita hwata wannan in ta sha kashin ruwa duk sai ta saki ko ka yi aiki da ita ba ka jin daɗin aikin. To. Yanzu daɗa da shi wanga in ka zo ka sa wanga, ko da ka yi aikin da shi kō da dà rani ne ka yi aikin, in ma kai, in damana ta zo gaba ɗai shī ƙara kerewa ma yakai, ya ji sanyin ruwa.

Int: Mm.
OA: To shi ne yanzu sai muka daɗa sai muka koma muna hauda shi.
Int: Mhm.
OA: E. Ka ji abin da ake sa…amma hakanga in ka ce wagga babba dumiya, wagga ƙarama dumiya, amma in ka yi kwampile hakanga sunansu duma.
Int: E.
OA: A'a. Asulinta Maraɗî ne. Duk ko in…yanzu in ka ga duma dai da ka ga duma sai ka ji an ce Maraɗî, daga ƙasa Maraɗî suka hito. Ko da ma wani ya zo ya koye su daga nan, ya kai su wani wuri, kâ ji an ce dai daga ƙasa Maraɗî sunka hita.

Int: Mm.
OA: Kuma yanzu in kama sun hita daga nan in sunka tai Paris, sunka tai Amerik, kâ ji an ce 'a daga Nijar suka hita'. Nijar kuma sai ce ma 'a' Nijar, ko kuma da an ce ma Nijar sai an ce ma ƙasa Maraɗî.
Int: E.
OA: Ni na zo na iske su ga tsohona tun ina da shekara goma sha biyar nike biya su ina ganin ana buga su ana buga su, ha aka zo aka, aka ce in zo, in zo in hwara da wanga. Da na hwara da wanga dan ƙarami wannan, aka koma aka ba ni wancan na icce ga ya can. Ga ya can saman nan sai na ɗauko ma shī ka ganē shi. In ɗauko shi ka gani yaakin na ƙare, wanga in hwara hawan wanga, *en soixante dix et neuf* na hwara hawanshi Arlit.

Int: Mm.
OA: Babana …ƙanen babana ne, shina…shina kwance bai da lahiya, kuma an kira mu wurin kiɗin suna, duka waɗanda, manya manya waɗanda muke biya su je su hau suka ce su ba su iyawa, ni ce ba dai kiɗi

© Boston University

ba, ni ce ku ba nì nī nì je in hau. Ni zo ni hau na hwara na hwara ya zo ya iske ina yi ya ce ‘a, Ummaru ashe ka iya wanga abun kake barinmu muna wah, mu… muna gajiya da haka’. Na ce ‘A’a yau ne dan sabo da ka…an ce an ce kowa ya zo ya hau kowa ya ƙiya na ce to ni ma yanzu na gani ni ma zani kwatantawa in hau in gani in nî iya. To, shi ne abin da suka riƙe abin da ni riƙe ga kaina shi ne ni riƙe kuma yanzu bisa da aikin nan da nike yi na bisa kaina, yau da gobe yau da gobe yau yanzu ga shi ha na zama, duk ya yi mini *maitriser* yanzu sai dai wani abu ya hwaɗo mini da kai ba aikin da aka koya muna ba.

Int: Mm.
OA: Sai dai ni in iba cikin nau kuma wanda, wanda, wanda aka gwada min kin yanzu ha ya ƙaru kuma ni kuma ha yanzu ni kuma ina ma ƙara *recherche* kin.

Int: Mm.
OA: Kama sai lokacin da akwai armammaki, ko wata salla ko kuma wata sabga wa…sabga dai kawai ta samari da ‘yan mata kawai sai a kira ku kawai ku tai kawai ku tai. Kama kuma yanzu ga damana, kama sabo da ba kaɗe-kaɗen buki ake ba kuma ba kiɗin arme a kai ba, yanzu sai ku dibi garuruwan da zaku tahiya kama yarinya da kuke so ku hidda sunanta sai ku je kama da damanan nan, kama in suka hito da gona, in aka hito daga gonakki daɗa sai ku zo ku sabka gidan yarinyan nan, to yau da marece kun sabka wajenta daɗa sai ta gaigaya ma abukkai, sai a gaigaya ma ‘yan mata a ce ai wane, wance ta yi baƙin makaɗa. Sai a zo daɗa a yi ta wasanni ko kwana biyu za a yi a yi ta wasanni kuma sai an ƙare nan wurin ba ku son ko dala komi ba ku so iyaka dai wasanni na zaku yi kwana dai kwana bi ne kuma a wuce gaba. Yanzu ke nan sai kaka ta yi, in kaka ta yi daɗa duk garin da ka je ka yi wannan sana’a sai ka je in aka hwara yankan abincin nan, aka hwara hidda abinci aka hwara hidda hatsi, komi da kaka ta yi daɗa sai ka zo ka sabka cikin garin sai ka ce to ka taho wurin barka da barka da arziki. To yanzu cikin awan nan kama wannan kaɗe kaɗe shi ne muke cewa kiɗin dâmmā kama wasa wasa kara haka. To in aka zo mai dame mai wasu ‘yan kuɗi ne duka dai in dala bi bi bi ke gare ki dai ke dai ki kawo dai ki tara ma wannan allashi a kawo gaban makaɗin nan shi ne sallama shi na kaka.

Int: Mm.
OA: To yanzu shi kama inda za ka *changement* kin kukan duma ya sauya duka ka yi magana da shi, ka ga da nan ne. Wânga shi ke zama nan wurin. Kana ganin wanga wurin ai duk ya dan gurje kaɗan ba he da yawa ba. To wagga ita ce na wurin. Wanga shi ne nan wurin. Ka gane shi kowane da nashi wuri. Kama yanzu nan in kana so sai in ce ma …Ka ga na ce ma Mansur da hannu guda ne. In ina son in sa hannu biyu …ke nan …ke nan duka dai duka dai tahiya su guda ne. Amma in ka ce ka … bugu biyu ne dai zaka yi. …Ka gani? “Mansur”. Ke nan bugu ukku ne “Laraba”. In ina so in sa wagga. Ka gani “Laraba” ka gani duka biyu ne. Mansur, duka, duka kiɗi *traditionnel* a ce wanga ma dai *traditionnel* ne, duka ko na kalangu ne, ko na ganga ne, ko na mine ne duka magana ce. Kama yanzu in ina so in kira mutumen, daga nan wurin in shina, in shina nan kusa sai in kira shi. Kama yanzu *grand frère* kina da ke nan zamne shina nan shina sauraren Radiyo, yanzu da na kira shi na ce mai ya zo, kama kai ne sai in kwatanta ma in ce wane taso ɗauko min abu kaza, wane taso ɗauko min abu kaza ka zo mu yi aiki kaza tare, da duma ne sai ka ga ya taso nan wurin ba zato ba tammaha ya zo ya ɗauko, ka ga dai ya shigo ɗaki amma ba ka san ni na yi mai magana ba ko wa ya yi mai magana. Ya ɗauko kawai sai ya zamna kawai mu zamna mu yi aiki. Ke nan yanzu ina iya yi maka wannan *essayer* kinka gani. …Yanzu kâ ganai.
Halilu: A kira a ce ka kawo ruwa. A kira a ce ana son tabarma za a azawa a yi wasa, a ka …a ce ana son kujera duk suna yi.

Int: Mm.
Halilu: Yanzu nan ya kirai ni da duma ya ce in zo, ya yi kirana ya ce “Halilu jikan Guga. Ni kakana Guga. Ya ce Halilu jikan Guga taho ina kiranka. Ni zo ya ce in ɗauko kazagge in kaɗa.
Int: Mm.
Halilu: Bayan haka ya ce in ɗauko mai kurkutu da duma. Ka su nan ni kawo.
OA: Ka gani? Magana ce.

Int: E.
Halilu: Kama yanzu nan, kana nan, kana, muna hili muna wasa wagga ba ta zo ba sai ka zo sai ka ce kawai ga kuɗi a buga kakin wance ta zo… ka jiya.
OA: E. Kawai buga mini taken wance in jiya?
Halilu: Ita kuma tana iya. In ta ji ba a ambace ka ba, ba ka nan tana yiwa ta zo ta yi magana ta ce mi ya sa …

OA: E. Mansur bai zo ba?
Halilu: … samari duka …dan wane bai nan ne ka yi haka? Wani abu kake so, bari a hidd…sai a hiddo wani abu a ba ka a ce ‘amshi ka buga in ji’. Ihhe, ka gani?
OA: Wannan zani buga muku tun wanda munka hwara aiki da shi. Ana ce mata gāɗa wadda munka sani ta manyan mata wurin arme, ita ce gada.
Halilu: Mm. Kiɗin uwa ɗiya.

OA: Kiɗin uwa ɗiya ke nan.
Halilu: Wadda ɗiyatta tana arme ana harkoki.
OA: Mu a can ƙasa Maraɗi. Ka san wajenku sai ku ce ‘tākùrētì’ ƙasa Dogondutsi sai a ce ‘takureti’. Mu ko wajenmu sai mu ce ‘gada’. Ƙasa Tawa sai a ce ‘tārai’. Ƙasa Agadas sai a ce ‘tarai’. Nan ko sai su ce ma mine ne hira nan ‘yētì- yētì ‘.
Int: Mm.
OA: Ka gani?
Int: E to e.

OA: Haka nan ne.To mu wajenmu sai mu ce gaɗa. To ka ji kiɗin gaɗa. Shi ne yanzu kama asa Maraɗi da ka ji ana wanga to.
Halilu**:** Arme ne ake yi.
OA: Arme ne ake.

Int: Mm.
OA: Da ka ji ma an hwara wannan. Da ma da ka zo kai makaɗi in dai arme ne ake wanga kiɗi shi ne zaka hwara sanyawa. Ni akwai nau wanda ni ƙirƙira. Ni akwai nau wanda ni ƙirƙira. Kama ni lokacin da ina tare da wasu yara cikin lakkwal kin Maraɗi ana ce mata *jardin d’enfants* ta yara hakanga. To zazzamne hakanga sai tsakanin abukkai da abukkai sai wani ya ce mini ‘ba ni ruwa.‘ Sai na ce ‘□’ā’, ka ga wannan hwa in kana samun *temps* kin wannan ka ga gyaran rawa ne. Sai ni runguma shi ina haka ‘ba ni ruwa, ba ni ruwa, a ba ni ruwa’ Ke nan yanzu sun maida shi waƙa. Ni kuma sai na zo na saurara sai na zo na gyara shi da duma. Da na zo na gyara shi da duma sai ina hakanga sai ina hakanga (*he is drumming*). To daga nan wurin sai muka yi *maitriser* muka mai da shi rawa. Yanzu in ka ga, kama in muka tai wurin buki sai ka ji an ce “kai a kaɗa mum ‘ba mu ruwa’”. Ke nan ko da …da ma an ce kai a kaɗa mum ‘ba mu ruwa’ ke nan an san kiɗin da anka ɗauko. To ni wanga kiɗi ni ni ƙirƙira shi ni ni

hiddo shi bakin ‘ba ni ruwa ƙanen Sani, a ba ni ruwa gidan mānī.’ To ka ji shi. Shi ne na sa ga duma. Sai na hauda.

Int: Mm.
OA: Wanga. Shi ne wanda dai ni san na hidda da kaina. Amma duk kaɗe kaɗen da ka ji muna yi, duka mun sauraresu ne ga manyanmu, duka da wanda ya koya muna da waɗanda suka koya muna mun saurare su ne. Kuma ka zo cikin gari kana kuma ka ji ana yi ko da da kalangu ne, ko da da ganga ce, in ka saurara yanda zaka yi ka zo ka yi *maitriser* kinshi ka juya bisa dumanka kai kuma ka yi. Mu yanzu duk, ka ga muna tahiya nan Yamai a na Yamai ma muna zuwa wurin arme, muna zuwa wurin suna. Kai hatta da yanzu samari suka shirma takkai, hatta da kai yanzu ka yi muradinmu wurin kiɗin duma hakanga, sai mu zo mu kwashi kayanmu mu tai mu, mu yi wasa bakin ƙohwa gidanka. Mu ji kawai jin daɗin rayuwa ne. Ke nan al’adu ne tun na da ba ka mance da su ba, kai kuma ka kirayo al’adakka, yanzu duk in kalangu ka gada sai ka yi *mélanger*, sai ka gama da kalangu a masu kalangu su zo su buga masu duma su zo su buga. Wane ne ya hi *difference* ciki zaka gani? A wane ni irin kiɗin ƙasakku zaku yi mini, sai mu buga ma takkai. Mm? Ko kuma in kama samari da ‘yan mata ne sai mu sai mu buga ma rawa ta samari da ‘yan mata kawai. Kama wani sareta, wani … ƴas sahabi, kama wani jarka hakanga, kama wani larab hakanga. Ko kuma kama irin raye rayen ga da ka ji ana yi muna muna *mélanger* cikin muna *mélanger* cikin *musique* haka kama wani a dumulmula, ko wani …mine ne ake cewa …kin gani kin gani tubarkalla duka kaɗe-kaɗe ne na galgajiya duka. Shi ne suke ɗauka suna mai …suna gamawa suna waƙoƙi da su yanzu. Yanzu da ka ji mutum in ya hwara waƙa da kayan kiɗin gargajiya sai ka ji sunanshi ya hwara hita.

Int: Mm.
OA: Yanzu Nasara ina zaka gwada mai *guitar*? Shi ya yi abu tai. A? Nasara ba ka gwada mai *batterie*, shi ya yi abu tai. Ba ka gwada mai *piano* shi ya yi abu tai. Amma sai mu zo da wannan sai mu zo duk abin da ya yi bisa *piano* kin nan sai mu zo canza mu yi mu samu mu ma mu ebi rabonmu ciki. Amma shi in ba shi ya zo ya koya ba, bai samun abin da zai iba cikin namu.

Int: E.
OA: Ka gani? Dan sabo da galgajiya tashin hankali ce. To dan haka in ka riƙe galgajiyakka dole ne ka ci anhwanin abukka. Wai. Ko kwanan gobe, ko kwanan gobe, dan yanzu haka ni ina nan, ina ganin mutane waɗanda suka yi *rendez-vous* da ni yau, dan sabo da wannan *rendez-vous* naku na ce a’a. Dan sai na ƙare da ku allashi na ce su ba ni zuwa ƙarhe bi ko zuwa ƙarhe ukku, mu haɗu istudiyo.

Int: Mm.
OA: Dan sabo da ka ga ƴan dandalin soyayya sun zo mun yi *contrat* da su sun ce in tai in buga musu a cikin istudiyo. In buga musu duma ko kalangu. Muka yi *contrat*. Eee masu *rap,* wannan *rafêye* su ma suna nan suna aiki suna jirana gidan Bature. Yanzu da na tashi daga nan, da mun ƙare aiki na tashi daga nan gidan Bature zani mu yi aiki tare da su.

To lalle dai kaɗan kaɗan alhamdulillahi ina samu.
Int: Mhm.
OA: Tun da ko yanzu cikin, cikin e cikin *etudiants* kin nan na *inibersite* ta bayan ruwa, babba inibersite ta, ta Nijar, dan ina da yaro, ina da yaro huɗu wanda ni koya ma duma. To amma ha yanzu ba su ida *maitriser* kin hannun ba sabo da bisa hannu ne amma muna nan muna aiki tare da su kaɗan kaɗan. Nan ma da kwana kaɗan ina jin wataƙila, sun ce mamu in Allah ya yarda ana sake kiranmu mu koma mu

hauda wannan aiki wanda munka yi dan sabo da a gwada ma manya zamu samu ko da wata bi ne ko da wata guda ne a samu a yi *maitriser* kin yara tun da yanzu mu yanzu dàjâ mun yi nisa. Dole yanzu mu samu na baya waɗanda zamu koya mâ. Tun da yau in kai ne gobe ba kai ne ba. To yanzu in ba ka da wani na bayan ka ke nan wanga kaya ɓacewa zasu yi. Kuma in suka ɓace ka gani ke nan sai dai a ce ‘a wane lokacin nan da wane da wane su ne ke buga su amma yanzu ka ga tun da ba su, yanzu ba a samu mai hawansu ba ya buga’. Ke nan an barsu nan wurin yanzu sai dai a yi ta kallonsu a tarihi. Ba mai ba mai izinin buga su. To amma in kana samun guda guda a nan cikin ƙasammu dai a Nijar in kana samun guda guda waɗanda zasu zowa suna koyo, ko da bai gwanance ba wata rana shi ne zaya zama gwani.